Global Protection Cluster
Groupe de Travail Protection Diffa

# TAKARKUN NEMAN BAYANAIDOMIN AYYUKAN JINKAI
# Jahar Diffa, Jamhuriyar Niger

## TSARIN KIYON LAFIYA

- Mata da kananin yara na samun zuwa Santocin kiyon lafiya a lokutta da kuma wuraren da aka tsara ?
- Abubuwan zirga-zirga da aka tanadar lokacin da ake takaita zirga-zirgarJama`a suna aikiyadda ya kamata ?
- Tsofaffi da masu nakasa na samun zuwa Santocin kiyon lafiya ?
- Akwai aikace-aikace domin masu renon ciki a asibitocin kiyon lafiya ?
- Akwai mata a cikin ma`aikatan kiyon lafiya a asibitocin ?Ya adadinsu yake ?Ko sun isa ?
- An samarda aikace-aikace da kuma Kawrarrunma`aikata a sashen kula da masu tabuwar hankali da daukar katakan kariya a asibitocin gwamnati ?
- Akwai wani tsari na bada rahoron bullar cutar da kuma bada shawarwari a ziyarciasibitocin ?
- A asibitoci , akwai wuraren da aka kebe inda mata, kananan yara ko sauran al`umma kan iya tattauna matsalolinsu a asirce ? Shin ko ma`aikatan asibitin sun damu su rufe sirrin ?
- Wadanne irin muhimman matsalolin ne kan hana mata da `yan mata zuwa asibitoci (Misali: nisa, tsadar abubuwan hawa, rashin mata masu duba marasa lafiya, al`adu , rashin kwararrun ma`aikata da sauransu ) ?
- Wadanda suka kamu da Ciwon Kanjamau, ko suna da masaniya akan aikace-aikachen sashen masu dauke da cutar ? Ana rufe sirrinsu ?
- Ana ba wa yara, mata da kuma mutane masu nakasa dama su bayyana ra`ayoyinsu akan samarda hanyoyin karfafa zuwa asiliti da kuma inganta wararen kiyon lafiya domin amfanin wadanda suka rasa matsugunninsu ko kuma iftila`i ya fada wa ?
- Wadanne irin shawarwari ne aka samu ?

- Akwai ma`aikatan da aka ba wa horo domin gano cuta, daukan matakan kariya, wayarda da kawunan al`umma, karfafa zuwa asibiti domin samarda ingantattar lafiya ?
- Akwai kwararrun ma`aikata dakekula da wadanda suka tsira da rayukansu wajen fashewar nakiya da kuma REG?

## SAMARDA KAYAN ABUNCI DA KUMA ABUBUWAN MORE RAYUWA

- Al`umma na samun zuwa Santocin rabon kayan abunci cikin sauki (Misali :nisa, inda ake iya isa can a kafa) ?
- Santocin na da nisa daga Sansanin Jami`an Tsaro ?
- Al`umma na jin cewa ingantattun bayanai akan wuri da kuma lokuttan rabon kayan abuncin sun isa ga kowa ?
- Ko an bayyana Santocin da wata alamar tantancewa domin saukin ganewurin ?
- Dabarun tantance masu zuwa neman kayan abuncin na da inganci ? An taba samun faruwar wani abu ?Misali : hatsaniya ?
- Jami`an rabon kayan na sanya kayan aiki ? Suna hulda kyakkyawa da yara ?
- Yana basu shawarwarikwarai?
- Sontocin nada barazanar rashin tsaro ga mata da `yan mata ?
- Wuraren na da barazanar rashin tsaro ga sauran rukunan al`umma (da ba mata da `yan mataba)?
- Idan akwai, wa abun ya taba shafuwa ?
- Ana tsari wajen rabo kayan domin su sami isa ga mata da `yan mata (misali : kebantaccen wuri domin su, layinsu daban, mata ma`aikatan rabon kayan), wacce irin matsala ce anka taba samu ?
- Ana tsari wajenrabon domin amfanin mutane masu nakasa ?
- Ana tsariwajen rabon domin amfanin tsofaffi/gajiyayyu ?
- Lokuttan da aka kebe domin rabon kayan nada gamsuwa/karbuwa ? sabanin haka, to me ne matsala ? (ko da idan daukar kayan na bata lokaci)
- Ko tsarin rabon kayan na da tanadin bada fifiko ga mutane masu bukata da musamman kamar tsofaffi , guramu, makafi, yara marasa galihu, mata masu ciki da kuma masu shayarwa ?
- Akwai changin alkamullan mata ko na kananin yara masu zuwa neman kayan abuncin ?

- Idan  akwai, raguwa ko kariaka samu ?
- Kayan abuncin da sukan samu yana da nauyin da sukan iya daukansa; ko sai sun biya kudin abun hawa ?
- An taba samun hadari ko hasara akan hanyarsu ta komawa gidajensu ?
- Idan mutum ya sami damuwa lokacin rabonkayan, ko akwai hurumin dake bashi dama ya nuna damuwarsa ?
- Ana saka mata, yara da kataimaka wajen adadin rabonkayan ?
- Akwai shawarwari domin inganta rabon kayan ?
- Matakan da ake dauka lokacin dokar-ta-baciko kuma d wuraren `yan gudun hijira, basu da hadari ga mata da `yan mata ?
- Wadanne irin matakai ne aka daukarwa al`umma domin yaki da rashin abunci/chimaka ?
- Matakan da ake dauka ga sauran rukunin al`umma (da ba mata da `yan mata ba)lokacin dokar-ta-baci ko kuma wuraren `y`an gudun hijira,  suna da hadari ?
- Ko mata na shiga shiraruwan  samarda abunci sabanin su yi aiki ? Idan ba haka ne, wadanne ne muhimman matsalolin da ke hana su shiga

## FANNIN SAMARDA ILIMI

- Akwai isassun Malamai ? Mene ne adadinsu ?
- Yara `yan makaranta na gamuwa da matsalolin rashin tsaro akan hanyoyinsu na zuwa da kuma dawowa daga makaranta ?
- Akwai makewayin yara maza da na `yan mata rarrabe a makarantu ?
- Akwai banbancinzuwa makaranta tsakanin yaran da iyayensu suka rasa matsugunni da kuma wadanda ke zaune a gidajen iyayensu sa asuli ? Idan akwai,  mene ne dalili ?
- Akwai banbancin zuwa makaranta tsakanin yaran da iyayensu suka rabu da kuma wadanda basu da masu  tsaya musu  ?Idan akwai,  mene me dalili ?
- Akwai matsalolin daukan yara a makaranta ko kammala karatunsu (Misali :rashi kudin makaranta, litattafai da sauran kayan aiki, tufafin makaranta, da sauransu) ?
- Akwai matsalolin wajen shiga harkar kula da lambu da kuma kiyon dabbobi ga`yara makaranta ?
- Malamai na kula da yara a cikin koyarwarsu ?

- Malaman na da horo akan matsalolin changin wurin zama ?
- Malaman kan iya gane yanayin cin zarafi, fyade, bautarwa da kuma rashin kula da yaran su kuma saka hannu da nunawa yaro inda zai je yakai kokensa ?
- Idan aka sami cin zarafi/fyade wa yaro daga daya daga cikin malaman, malaman kan iya nuna shi
- Suna da horo akan koyarda kyakkawar tarbiya da kuma illarhoron bada kasha ko aiki mai tsanani ?
- Malamai da sauran ma`aikata a makaranta sun san da dokokin yin biyayya ?
- Malamai da dalibai ko sun san yadda ake daukanmatatan kariya da kuma inda ake kai rahoton cin zarafi ?
- Ko an saka dabarun gane abubuwan fashewa a koyarwar yau-da-kullum?
- An saka dalibai a cikin jerin masu bada shawarwari dominsamarda ingantaccen ilimi wa wadanda suka rasa matsagunnansu da kuma wadanda iftila`I ya fadawa ?

## SAMARDA RUWAN SHA DA MAKEWAYI MASU TSABTA

- Mata na samun ruwan sha masu tsabta ?
- Yara na samun isassun ruwan sha masu tsabta ?
- Mata, yara, tsofaffi da masu nakasa na samun isassar fadakarsuwa akan makewayi na zamani ?
- Akwai makewayi a makaranta ; wanda keda kariya domin yara da kuma mata ?
- Akwai intantaccen wurin samarda ruwan sha domin yara ?
- Wadanne irin wuraren samar da ruwan sha ne ake da shi (misali : rijiyar laka, rijiyar siminti, dabaru irinna FPMH (indien), bohol, pampo (SEEN) , tabki, marmaro da dai sauransu) ?
- Wadanne irin dabarun adana ruwan ne ake amfani da su ?
- Wadanne irin wuraren samar da ruwa sha ne suka fi sauki ga gajiyayyu da kuma musakai ?
- Akwai makewayi na zami dominmata da yara `yan mata a gefe daya maza da yara `yan maza ?
- Akwai kungiyoyin samarda tsabtatattunruwan sha ?
- Yaushe ne karshe suka yi taron tattaunawa ?
- Wajen samarda makewayi, ko an kiyaye ka`idodin samar da kariya ga mata da kananin yara ?
- Makewayin gargajiya irin na latirin yana da dadari ga yara ?

- An taba samun wani hadari ?
- Zuwa wajen samarda ruwan sha yana da hadari ko wuya ga yara ?
- A dalilin zuwa neman ruwa , an taba samun hadari misali a makaranta, gidan aboki ko a wasu wuraren ?
- Tsofaffi da masu nakasa na samun yin amfani da makewayinazamani ?
- Mata ko `yan mata wanne makewayi ne suka fi jin natsuwa da shi , na zamani ko na garagjiya ?
- Wacce irin matsala ce suka taba cin karo da ita ?
- Ko akwai wata shawara domin inganta samarda tsabtatattun ruwan sha da kuma makewayi ingantacce ga mutanen da suka rasa matsugunnansu ko wadanda wani iftila`i ya fada kansu ?
- Samarda kayan tsabtar mata ya yi daidai da bukatun mata da `yan mata ?
- Ko akwai wata shawara domin samarda ingantatttun kayan kula da tsabtar mata ?
- Akwai matakan da ake daukana samarda makewayi domin amfanin mata da yara a cikindare ?
- Akwai mashayar ruwan rarrabe na mutane da kuma dabbobi ?

INGANTACCEN WURIN ZAMA

- Wurin zaman yana zaunarda iyali ; ya cika ka`idodin kare mutunci mata da `yan mata ?
- Wadanne irin matsaloli ne matan da `yan matan ke fuskanta a gidajensu ?
- Bayyana muhimman matsaloil guda uku da mazauna gidaje ke fuskanta (misali: yawan jama`a ko rashin kariyar mutunci, rashin tsaro, rashin tsabtatattun ruwan sha, rashin issassun kayan dafuwar da gyaran abunci, tsadar kudin haya, halayyar masu gidagen haya) ?
- Ko yana da wuya ga wadansu rukunin Jama`asusami wurin zama ko gidan haya ? Idan haka ne, to mene ne dalili ( Misali : saboda macce ke jagorancin gidan, yara ke jagorancin gidan, tsirarrun kabilu ne ko addini) ?
- Ko mata nada damar mallakarfili ?
- Ko mata na iya gogon gida?
- Akwai shiraruwa na musamman da aka kebe domin samarda filayeko gidaje na dindin ga `yan gudun hijira a sansani ?Ko `yan gudun hijirar na da damar mallakar fili ko gida ?tabbacinmallakar gidan yana da garanti ?

- Akwai shiraruwa na musamman da aka kebe domin samarda filaye ko gidaje na dindin ga wadanda aka mayar daga wata kasa ? Ko suna da damar mallakar filaye ko gidaje ? Ko ingancin mallakar garanti ?
- Akwai tallafin ko ihsani da aka bawa wadanda suka rasa gidajensu ko aka biya diya ?Idan akwai, Ko wadanda abun ya shafa suna da masaniya ?Iyalai nawa suka nema? Nawa suka sama ?
- An kula da magidanta masu mata fiye da daya da kuma yara masu yawan shekaru wajen rabon wurarenzama ?